RESOLVE NETWORK

TAKARDAR BAYANI

# FAHIMTAR "GIDA" A SHIRIN SAMAR DA ZAMAN LAFIYA

Samar da zaman lafiya fage ne da ke samun ci gaba a tsakanin al'ummomin da ke fama da tashe-tashen hankula a yankin Kudancin Afirka, sannan ya kasance ɓangare mai muhimmanci na shirye-shiryen masu ba da tallafi na ƙasashen waje da dama. Wannan bunƙasa ya zo da ruɗani game da yadda tsarin shirye-shiryen samar da zaman lafiya suke da kuma yadda za a auna su, sannan ya zo da waɗansu sababbin ɓangarorin da aka yi matsaya game da su. Kai tsaye, duk waɗansu ma'aikata da ke kowane matakin shirin samar da zaman lafiya yanzu sun fahimci muhimmancin shirye-shiryen da suka shafi magance musabbabin tashe-tashen hankula daga tushe da nau'ukansu tare da ƙarfafa mutane da ƙungiyoyi domin bin matakan gargajiya na samar da zaman lafiya "waɗanda ba su tauye haƙƙin 'yan adam ba" waɗanda suke mayar da hankali kan dabarar shawo kan matsala daga sama domin samun zaman lafiya. Wannan takarda na ɗauke da tsakuren sakamakon bincike daga Rahoton Binciken RESOLVE wanda ya shafi bitar ayyukan da suka gabata masu tarin yawa da kuma nazarin ƙwaƙƙwafi game da lamura guda huɗu da suka kasance manyan misalan matakan samar da zaman lafiya na gargajiya bayan samun tashe-tashen hankula a Kudancin Afirka. Rahoton ya yi iƙirarin cewa "na gida" a cikin shirin samar da zaman lafiya na gida na nufin ilimin gida na sababban tashe-tashen hankula da sauye-sauyensu, da kuma ma'anar zaman lafiya da aka samar da shi bisa fahimtan gida da ke da bagire taƙamaimai. Wannan ba dole ne ya ɗauki ma'anar ƙarfafa wa ma'aikata da hukumomi "'yan gargajiya" ba (wanda ya kasance rukunin da ake ƙalubalanta, a kowane bagire). Sanna ba ya nufin a taƙaita mahangar kan sabubban samuwar tashe-tashen hankula da ma'aikatan samar da zaman lafiya da matsayinsu bai kai na matakin ƙasa ba wanda hakan ke tasiri yayin auna yadda sauye-sauye a matakin ƙasa da ƙasa-da-ƙasa ke tasiri a kan ƙalubalen zaman lafiya da ake fuskanta a matakin karkara (da kuma yayin da aka juya zancen).

Masu ba da tallafi da ma'aikatan samar da zaman lafiya na ƙasa-da-ƙasa sun fi samun nasara yayin da suka yi aiki tare da sanin cewa duk waɗanda suke iya tasiri kan sha'anin samar da zaman lafiya (ma'aikata a matakin ƙasa ko karkara, da kuma masu ba da tallafi daga waje, "ƙwararru," da kuma masu zartarwa) duk suna da manufofinsu, sannan ƙoƙarin samar da zaman lafiya da ke aiki a matakin da bai kai na ƙasa ba wanda kuma ke aiki tare da mutane daga karkara ba dole ne kai tsaye su kasance amintattu ba waɗanda al'umma suke aminta da su sakamakon kasancewarsu na "gargajiya" ba. Sannan dole ne ma'aikata a matakin ƙasa-da-ƙasa su kasance masu karɓar sauyi tare da buɗe ƙofofin haɗin gwiwa da ma'aikata daban-daban daga karkara, ciki har da waɗanda ba su cimma abin da ake buƙata a matakin ƙasa-da-ƙasa ba game da yadda ya kamata ma'aikacin da za a haɗa kai da shi daga karkara ya kasance (sau da dama, dattijo, namiji, sannan "ɗan gargajiya").

Domin ƙarin bayani, a duba: Kendhammer, Brandon, da Wyatt Chandler. *Fahimtar "Gida" a Shirin Samar da Zaman Lafiya*. RESOLVE Network, 2021.

## MUHIMMAN TAMBAYOYI DA MUHAWARORI

Kasancewar akwai matuƙar buƙatar ingantattun matakan samar da zaman lafiya da kuma ƙaruwar buƙatar samun bayanan yadda ake gudanar da lamura daga ɓangaren masu ba da tallafi da abokan haɗin gwiwa na waje, rahoton ya yi bitar ayyukan da suka gabata masu tarin yawa game da matakan samar da zaman lafiya na "gargajiya" tare da manufar taimaka wa mahukunta wajen fahimtar damarmaki da ƙalubale sauye-sauyen da ke cikin lamarin. Kai tsaye ya tunkari muhimman tambayoyi da muhawarori guda huɗu da suka shafi ingancin amfani da matakan samar da zaman lafiya na gida ta hanyar mayar da hankali musamman a kan misalan da suka shafi Kudancin Afirka.

1. **A ina ake samun "gida" a cikin "samar da zaman lafiya na gida"? Waɗanne mutane ne da wurare ake ɗauka a matsayin na gida (sannan mene ne dalilin hakan), sannan ta yaya ma'anoni mabambanta na gargajiya a sha'anin samar da zaman lafiya ke nuni ga cewa waɗansu shirye-shiryen sun fi samun nasarar samar da zaman lafiya mai ɗorewa sama da saura?**

2. **Waɗanne nau'ukan dangantaka ne za a iya samu a tsakanin matakan samar da zaman lafiya "waɗanda ba sa tauye haƙƙin 'yan adam"/na matakin ƙasa da kuma na gargajiya, sannan waɗanne nasarori da ƙalubale ne za a iya fuskanta yayin "haɗa hanyoyi biyu" domin samar da zaman lafiya?**

3. **Wace rawa ce ta fi dacewa masu ba da tallafi da ƙungiyoyi na waje su taka domin tallafa wa shirin samar da zaman lafiya na gida da kuma ayyukan masu samar da zaman lafiya na karkara, sannan mene ne damarmaki da ƙalubalen da ke ƙunshe a dukkannin sassan biyu?**

4. **Ta wace hanya ya fi dacewa mu yi auna datare da ƙalailaice matakan samar da zaman lafiya na gida sannan a samar da hanyoyin da suka fi dacewa ta la'akari da dacewarsu da bagiren gida?**

# DARRUSAN DA AKA KOYA DA SHAWARWARI GAME DA ƘA'IDOJI

**Bayani game da "gargajiya" a bagiren samar da zaman lafiya ba abu ne mai sauƙi ba, sannan ma'anar da aka yi amfani da ita na iya yin tasiri mai girma game da sha'anonin samar da zaman lafiya da sakamakonsu.**

Rashin samu tsarin da an yarda da shi game da ma'anar "gida" a mahalli daban-daban (ko a cikin wuri ɗaya), yana haifar da cin karo da juna wanda na iya haifar da matsaloli yayin da rashin fahimtar ta shafi raba kayayyaki da samun ɗaukaka. Sau da dama, mafita game da wannan matsala da ta shafi ma'ana ita ce samar da bayyanannun ƙa'idoji da suka shafi tsare-tsare ta la'akari da ilimin da ake da shi game da wani yankin da tashin hankali ya shafa. Wannan ilimi na gida bai kasance mai sauƙi ko kuma mai sauƙin samarwa ba (musamman ga masu ba da tallafi na waje), da gwamnatocin ƙasashe, masu hannu cikin tashe-tashen hankula, da al'ummomi a karkara, duk suna da muradansu waɗanda za su samar da sauyi ga bayanan da za a fitar.

**Lamarin auna zaman lafiya a gargajiyance dole ne ya kasance mai karɓar sauye-sauye tare da la'akari da yanayi.**

Kamar yadda ayyukan da suka gabata suka nuna, idan ya kamata ne mahukunta a gargajiyance su samar da ma'anar zaman lafiya na gargajiya, to abin da ke buƙatar ingantawa ba sakamako ba ne, sai dai shi kansa matakin aminta da buƙatar samun wannan gudummawa, fifita karɓarta, da kuma amfani da ita domin yanke hukunce-hukuncen da suka shafi mahukunta a matsayin abokan haɗin gwiwa sannan mamallaka. Zaɓen abokan haɗin gwiwa da suka kasance masu ido da karɓuwa a karkara (musamman ga ƙungiyoyin da manyan mutane a gida ba za su iya kaiwa gare su ba) sama da waɗanda suka kasance a shirye, masu cikakken ilimin gudanarwa na iya haifar da ƙaruwar tsadar gudanarwa amma kuma zai iya taimakawa ga samuwar matakan samar da zaman lafiya mafiya inganci yayin da tafiya ta yi tafiya.

**Mutane daga waje na iya taka rawa ga sha'anin samar da zaman lafiya a gida, sannan ya kamata su yi hakan.**

Tana iya yiwuwa a samu buƙatar mutane daga waje su waiwaici ƙa'idojinsu da matakanku a kuma yi musu kwaskwarima domin aiki tare da mutane a karkara domin magance bambance-bambancen da ke kawo tasgaro ga shirye-shiryen haɗin kai a karkara, amma dole ne manufar a koyaushe ta kasance ƙoƙarin samar da haɗin guiwa. Tashe-tashen hankula a matakin karkara na da tasiri a matakin ƙasa (haka ma abin yake yayin da aka juya batun), sannan ƙananan abokan haɗin gwiwa daga karkara ba dole ne a koyaushe su samu hanya ko ƙwarewa da ake buƙata ba na iya shawo ƙalubalen da suka shafi kayan aiki da kuma musamman siyasa yayin ƙoƙarin haɗa matakin karkara da na ƙasa. Mutane daga waje waɗanda za su iya shawo kan waɗannan ƙalubale suna da matuƙar muhimmanci a sha'anin samar da zaman lafiya a karkara wanda idan babu su za a sha wahala ko kuma ma ba zai yiwu ba baki ɗaya.

**Tsarin "haɗa hanyoyi biyu" ga lamarin samar da zaman lafiya na nuni da hasken samun nasara, amma ba kowane abu ba ne ake iya "haɗa hanyoyi biyu" cikin sauƙi.**

Shaidar sanya waɗansu abubuwa na gida a cikin matakan samar da zaman lafiya da ba sa tauye haƙƙin 'yan adam yakan kasance ya haɗa abubuwa sama da guda. Yawanci gawurtattun tsarin haɗa hanyoyi biyu domin ƙarfafa gwiwa a karkara a matsayin wani mataki na kauce wa nau'in tsarin samar da zaman lafiya da ba ya kiyaye haƙƙin 'yan adam, yana haɗa zaɓuɓɓukan da suka shafi al'ada tare da kauce wa matsaloli. Bincike ya nuna cewa yayin da ma'aikatan samar da zaman lafiya na ƙasa-da-ƙasa suka kauce wa ra'ayoyinsu na rayawar zuci sannan suka rungumi ilimin da ya fito daga matakin karkara kuma suka ƙarfafa shi, to ƙalubalen da za su haifar kaɗan ne, alhali alfanun kuma yana da yawa. Tsarin haɗa hanyoyi biyu na samar da zaman lafiya da suka fi dacewa su ne waɗanda suke darajanta alaƙar haɗin gwiwa tsakanin karkara da ƙsa da kuma karkara da karkakara, sannan suke bin tsari mai kyau wajen rufe giɓin da ake da su.


## RESOLVE NETWORK

Bincike Mafi Kyau | Tsararrun Matakai | Ingantattun Dokoki Game da Hatsaniyar Ra'ayin Wuce Gona da Iri
www.resolvenet.org | @resolvenet

*Ra'ayoyin da aka bayyana a cikin wannan rubutu na marubutan ne. Ba dole ne su wakilci ra'ayoyin RESOLVE Network ba, ko abokan haɗin guiwar da aka ambata waɗanda suka taimakawa wajen wallafa wannan rubutu, ko Hukumar Zaman Lafiya ta Amurka, ko duk wata hukuma ta gwamnatin Amurka.*

RESOLVE na ƙarƙashin Hukumar Zaman Lafiya ta Amurka, tana ɗorawa a kan aikin Hukumar wanda ta shafi tsawon shekara goma tana yi, wanda ya shafi aiki tuƙuru ga yankunan da tashe-tashen hankula suka shafa.

RESOLVE na amfani da wannan dama wajen godiya ga Hukumar Raya Kasa da Kasa ta Amurka (USAID) dangane da gudummawarta ga wannan rahoto da kuma Binciken RESOLVE na Jami'an Al'umma Masu Makamai.